*Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 015 (Pg. 166-175)*

# Kalubalen da Nazarin Al'adun Hausawa ke Fuskanta a Tsarin Ilimin Nijeriya

**Hassan Salihu**
*hassansalihu927@gmail.com*
*07068637973*
Department of Arts Education
Hausa Section
Federal University of Education, Kontagora

**A'isha Abubakar Giwa**
*aishag624@gmail.com*
*08036510315*
Sashen Koyar da Hausa
Kwalejin Ilimi ta Minna, Jihar Neja

**Muhammad Tukur Tanko**
*mtukur@gmail.com*
*07065915934*
Sashen Koyar da Hausa
Kwalejin Ilimi ta Minna, Jihar Neja

***Tsakure***

*Wannan takarda an yi bayanin ƙalubalen da nazarin al'adun Hausawa ke fuskanta a cikin tsarin ilimin Nijeriya. Manufar binciken ita ce fito da ƙalubalen da Hausa da al'adun Hausawa suke fuskanta da nufin yin hannunka mai sanda ga masu ruwa da tsaki. An yi amfani da dabarar nazarin wallafaffun littafai da shiga kafar intanet da tattaunawa da wasu mutanen domin tattaro bayanai. Kasancewar kowane bincike na zamani akwai mizanin da ake ɗora shi domin auna karɓuwa ko kuma rashinsa Saboda haka an ɗora wannan bincike a kan ra'in adana al'adu. Binciken ya ga dacewar wannan ra'i wajen aiwatar da wannan bincike. Daga cikin sakamakon da ka gano shi ne tilasata amfani da harshen Turawa da al'adunsu su ne illar da nazarin al'adun Hausawa ya fuskanta. Haka kuma an gano ɗabi'un wasu Hausawa ʽyan boko da kuma malaman Hausa sun taimaka wajen dakushe martabar al'adun Hausawa. Daga ƙarshe binciken ya ba da shawarwarin yadda za a magance ƙalubalen da al'adun Hausawa ke fuskanta.*

***Fitillun kalmomi:*** *Ƙalubale, Al'adu, Hausawa, Nazari, Hausa, Turanci*

## Gabatarwa

Masana ilimin harshen Hausa sun ɗora nazarin Hausa bisa wasu sassa guda uku, kuma kowane bangare an ba shi kashin kansa. Amma dukannin fannoni suna da'ira a tsakaninsu. Ma'ana suna yi wa juna shigan giragizai inda ake samun masana da manazarta suna ta ƙoƙarin faɗaɗa bincike domin zaƙulo da fito da sabbin abubuwa waɗanda za ya kyautata irin kallon da wasu mutane suke yi wa harshen Hausa, waɗannan ɓangarori su ne ɓangaren Harshe da ɓangaren adabi da kuma ɓangaren al'ada. A wajen gudanar da wannan nazari akwai

ƙalubale da suke fuskanta a cikin tsarin ilimi na Nijeriya. Dalilin haka ya haifar da salwantar wasu al'adu kyawawa da ya dace a ce an adana su ana koyar da su ga na baya domin bunƙasar al'umma baki ɗaya. Ƙalubalen da nazarin al'ada ke fuskanta ya hana wannan fannin ci gaba musamman a wannan ƙasar ta Nijeriya. Daga cikin abubuwan da suka kawo cikas ga ci gaban nazarin al'adun Hausawa a fagen ilimin Nijeriya su ne irin kallon da malaman addinin ke yi wa wannan fage, da kuma yadda gwamnati da ƙi ba wannan fanni muhimmancin da ya dace, da halaye da ɗabi'un wasu malamai masu koyar da wannan fanni da kuma yadda ita kanta al'umma take kallon wannan ɓangare. Babban umulhabasa'isan wannan ƙalubale shi ne tasirin zuwan Turawa ƙasar Hausa da kuma cusa harshensu da al'adunsu a cikin manhajar ilimin Nijeriya. Wannan nazari zai mayar da hankali ne a fannin nazarin al'ada tare da fito da ƙalubale da fannin yake fuskanta a tsarin ilimi na ƙasa sannan mukalar za ta ba da shawarwari a akan yadda za a shawo kan waɗannan ƙalubale domin inganta nazarin wannan fannin.

## Manufar Bincike

i. Babbar manufar wannan bincike ita ce fito da irin ƙalubale da nazarin al'adun Hausawa ke fuskanta a fannin ilimin Nijeriya.
ii. Yin hannunaka mai sanda ga masu ruwa da tsaki a fannin ilimi da kuma ɓangaren al'adun Hausa domin kawo gyara.
iii. Faɗakar da Hausawa muhimmancin al'adunsu na gargajiya da kuma nuna buƙatar adana su saboda amfanin na baya.
iv. Nuna matsayin al'adun Hausawa da irin gudummuwar da za su bayar wajen ilimantarwa da wayar wa jama'a kai a harkokin rayuwa na yau da kullum.
v. Fito da hanyoyin da za a bi waɗanda suka dace domin kawo gyara a cikin harkokin al'adun Hausawa na gargajiya. Wata manufa ita ce fayyace matsayin Hausa da al'adun Hausawa a idon `yan kallo domin fitar da su daga cikin duhun da suke ciki.

## Dabarun Gudanar da Bincike

Hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan bincike sun haɗa da :

1. Nazarin wallafaffun littattafai da kundayen bincike masu alaƙa da wannan bincike.
2. Nazarin muƙalu da mujallu da ƙasidu.
3. Saurararon jawabai da aka gabatar tarurruka na ilimi a kan al'adun Hausawa a gidajen rediyo da talabijin.
4. Ziyarar kafafen intanet domin nadar bayanai a kan abin da ya shafi batun da ake bincike a kai.
5. Hira da tattaunawa da masu ruwa da tsaki a kan harkokin ilimi da al'adun Hausawa.

## Ra'in Bincike

Ra'in bincike hanya ce da ake bi wajen gudanar da aikin bincike. Ra'in shi ne yake yin jagora wajen ganin haƙa ta cimma ruwa

a ƙarshen bincike, kasancewar in za a yi rubutu na ilimi sai an ɗora shi kan wani mizani na auna mahangarsa wanda ya dace da wata mazhaba na wani ko wasu manazarta. Yin hakan zai nuna mazhabar da karɓu a turbar bincike. Dangane da haka ne aka ga ya dace a ɗora wannan aiki a kan ra'in adana al'adu da ci gaban al'umma (Cultural Sustainability Theory) Wannan ra'i yana magana ne a kan cewa idan al'umma ta samu ci gaba dole ne a kare al'adunta domin gudun ka da su salwanta (Ado, 2017:78). Wannan ya yi daidai da matsayin da harshen Hausa da al'adun Hausawa suka samu a duniya. Bunza, (2022:8) ya bayyana cewa harshen Hausa yana matsayin harshe na goma sha ɗaya (11) a cikin harsunan duniya, wanda ke da mutane masu magana da harshen fiye da miliyan ɗari da hamsin. Bugu da ƙari, cikin harsunan Afrika Larbci ne kawai ke gaban Hausa da mutane miliya 522. Don haka, adana al'adun Hausawa wani abu ne muhimmin kamar yadda Yakasai, (2014) ya bayyana hanyoyin da aka bi wajen adana al'adun Hausawa wanda suka haɗa da rubutu da waƙe-waƙe da tatsuniyoyi da labarai da wasa da kacici-kacici da sauransu. Da wannan aka ga dacewar a ɗora aikin a kan wannan ra'i saboda yana bayanin hanyoyin da za a inganta al'adun Hausawa a cikin harkokin koyarwa, wanda hakan zai taimaka wajen magance ƙalubalen da nazarin al'adun Hausawa suke fuskanta a mizanin ilimi na ƙasa.

## Ma'anar Al'ada

Kalmar al'ada ararriyace daga harshen Larabci. Da Hausawa suka aro kalmar sai suka yi mata kwaskwarima yadda za ta dace da lafazinsu. A luggar Larabci, al'ada na nufin abin da aka saba yi ko ya saba wakana aka rigaya aka san shi. Masana da dama sun yi ƙoƙarin bayyana fahimtar su akan wannan kalma. Bunza, (2006) ya ce, "Al'ada tana nufi dukkanin rayuwar ɗan'adam tun daga haihuwa har zuwa kabarinsa". A ko'ina mutum ya sami kansa duk wata ɗabi'a da ya tashi da ita tun daga farkon rayuwa ya tarar a wurin da ya rayu, ko yake rayuwa, ita ce al'adar da za a yi masa hukunci a kai. Babu wata al'umma da za ta rayu a doron ƙasa face tana da al'adar da take bi, kuma da ita ake rarrabe ta da wata da ba ita ba. Shi kuwa Umar, (1985) cewa ya yi, "Al'ada ita ce sababbiyar hanyar rayuwa wadda akasarin jama'a na cikin al'umma suke amfani da ita. Al'ada ita ce hanyar rayuwar ɗan'adam, wato kowace al'umma tana da irin tata al'ada. Wannan hanyar rayuwa a cewarsa ta shafi yanayin zaman mutane da tunaninsu da iliminsu da fasaharsu da duk wani abu da ya shafi rayuwarsu ta yau da kullum tun daga haihuwa har zuwa mutuwa (Yakasai, 2012). Al'ada ta kasu kashi biyu, akwai al'adun gargajiya da kuma al'adun zamani. Al'adun gargajiya su ne al'adun da Bahaushe ya gada tun shekaru aruru kuma aka san shi da su. Bunza, (2006) a tasa fahimtar al'adun gargajiya su ne duk wata al'adar Bahaushe da yake jin shi ke da ita tun fil-azal kuma babu wata al'ada da ta yi naso a cikinta gaba ɗaya.

## Waiwayen Karatun Hausa a Cikin Ilimin Bokon Nijeriya

Masana da manazarta da dama sun tofa albarkacin bakinsu a kan lokacin da aka fara shigar da karatun Hausa a cikin tsarin ilimin

bokon Nijeriya. Daga cikinsu akwai Bakura, (2018:45) wanda ya bayyana cewa, karatun Hausa a cikin boko ya samo asali ne daga Turawa `yan buɗe ido waɗanda suka wallafa littattfai da suka shafi nahawun Hausa da ƙamus da wasu tatsuniyoyi da labarai da suka danganci ƙasar Hausa da al'adun Hausawa. Haka kuma sun tattara adabin baka na Hausa suka mayar da shi a rubuce. Bunza, (2018:4) ya jaddada cewa, ko da Turawa suka shigo ƙasar Hausa sun tarar da Hausawa da wayewar kai da ilimi na rubutu da karatu a cikin ajami. Hakan sai suka fara ƙarfafa fassara da rubuce-rubuce wanda suka ba da damar kafa harsashen farko na karatun boko a Nijeriya da suna "Yaƙi da jahici".

Daga wannan aka fara har Hausa da al'adun Hausawa suka kai matsayin da suke a yau. Inda ake gwagwarmaya da Hausa da al'adun Hausa a matakan ilimi daban-daban. Bunza ya ƙara da cewa karatun Hausa ya samu damar ƙetare Nijeriya inda Hausa ta shiga sahun ilimi a wasu Jami'o'i daban-daban sannan take da manyan shehunan malamai ma su yi mata kariya. Amma duk da haka nazarin al'adun Hausawa na fuskantar ƙalubale a fagen tsarin ilimin Nijeriya. Wannan ƙalubale shi ne maƙasudin wannan takarda da zummar yin hannunka mai sanda domin tada masu barci ko angaje su gano matsayin harshen a cikin tsarin ilimin Nijeriya. Musamman idan aka yi la'akari da cire Hausa da hukumar Jarabawa ta WASSCE ta yi a matsayin darasin tilas ga ɗalibai (Adeyanju, 2019:23).

**Ƙalubalen Nazarin Al'adu A Tsarin Ilimin Nijeriya**

Nazarin al'adun Hausawa a makarantun Nijeriya yana fuskantar wasu ƙalubale da suka yi tarnaƙi suka hana shi ci gaba, duk da muhimmancin da al'adun Hausawa suke da su wajen cusa tarbiyya ga matasa da kuma samar da hanyoyin dogaro da kai. Al'ummar Hausawa mutane ne masu alfahari da al'adunsu kyawawa waɗanda suka taimaka wajen ci gaban ƙasar Hausa (Sallau, 2018). Daga cikin ƙalubalen da koyar da al'adun Hausawa ke fuskanta akwai:

1. Tilasta amfani da harshen Ingilishi a Makarantun Sakandire: Koyar da al'adun Hausawa yana fuskantar matsala a matakin ilimi na firamare da sakandire duk da dokar ƙasa ta amince a koyar da harshen uwa a matakin aji 1-3 (FRN,2013). Harshe na ɗaya daga cikin abubuwan da al'umma ke amfani da shi wajen kaucewa salwantar al'adunsu (Yakasai, 2012:37). Kasancewar harshe shi ne maƙunshin al'ada rashin amfani da harshen Hausa ya daƙushe ci gaban al'adu a makarantun sakandire. Bunza, (2007:5), da Ntuli & Mundau, (2024) sun bayyana cewa Turawan mulkin mallaka sun tilastawa Hausawa koyon harshensu a makarantu har ana ƙyamar harshen Hausa da al'adun Hausawa. Fafunwa, (1992) ya tabbatar da cewa ci gaba da amfani da harshen Ingilishi a makarantu yana daga cikin illar da Turawa suka yi a tsarin ilimin ƙasa. Wannan ba ƙaramin illa ya yi wa

koyar da Hausa da al'adun Hausawa ba. Domin Tilasta magana da harshen Ingilishi da aiki da shi da mu'amala da shi da aka yi a makarantunmu a lokacin Turawa ya haifar da wata guba a zuciyar ɗalibai wanda har yanzu tana nan; inda suke kallon duk wani wanda bai iya Ingilishi ba a matsayin raggon ɗalibi. Sani, (2025) ya bayyana cewa tilas ne mutane su gane cewa Turanci yare ne kamar sauran yaruka fahimtarsa ko kuma iya magana da shi ba shi ne ilimi ba, ko basira waɗannan abubuwa ba su da dangantaka da harshen Turanci. Wannan ya yi sanadiyyar wasu ɗalibai na ƙyamar magana da harshen Hausa da al'adun Hausa, sannan kuma iyaye sun ɗauka cewa idan yaransu sun iya Turanci to, sun sami ilimi ke nan. Turanci shi ne mizani da ake amfani da shi wajen auna ilimin kowanne dalibi, wannan kuwa ba ya rasa nasaba da ɗaukar harshen Turanci da Nijeriya ta yi a matsayin harshen ƙasa (Niyi, & Apokere & Salihu, 2025). Harshen Turanci shi ne harshen da ya ke da martaba a idon `yan Nijeriya, yayin da harshen Hausa ya ke da ƙaramin matsayin a ɓangaren ilimi. Sai an sauya wannan tunani domin manyan ƙasashe da suka ci gaba da harshensu suke amfani a fagen ilimi. Ƙasashe irin su Amurka da Chana da Faransa da sauransu duk da harshensu suke amfani, (Bunza, 2018;10). A Nijeriya duk wanda ya nazarci harshen Ingilishi zai riƙa bugun gaba da ganin cewa shi ya waye, wannan yana da illa ƙwarai da gaske wajen nazarin al'adun Hausawa, inda ake kallon duk wanda ya nazarci al'adun Hausawa kamar wanda bai waye ba. Duk da haka Bunza, (2022) ya jaddada cewa babu kasawa ga karatun Hausa da al'adun Hausawa. Wannan ya haifar da kallon rainin wayo ga ɗaliban Hausa da malamansu

2. Kutsen baƙin Al'adu: Wannan yana ɗaya daga cikin abubuwan da suke ci wa koyo da koyar da al'adun Hausa tuwo a ƙwarya; Huasawa suna yi wa Turawa kirari da, "Kusa baƙin dole" zuwansu ƙasar Hausa ya yi sanadiyar samun wasu baƙin al'adu waɗanda suka saɓa wa al'adun Hausawa. Turawa sun cusa wa Hausawa wasu al'adunsu tare da amincewa da duk wani wanda ya yi buki bai yi koyi da su ba tamkar ya kasa ne KAmin, 2015). Duk wani buki da za a gudanar sai an yi wasu baƙin al'adu kamar *Oktai party* da *Dinner* da *Ladies Launcheon* da sauransu. Wannan ya sanya wasu kyawawan al'adun Hausawa na bukin aure ko haihuwa suna ƙoƙarin ɓacewa. Duk kuwa al'ummar da ta bari al'adunta na gargajiya suka salwanta, wannan al'umma ta rasa abin dogaro da alfahari da za ta bar wa na baya (Usman, 2014:10). Dogaro da baƙin al'adu zai taimaka wajen tarwatsa tarbiyyar Bahaushe, wanda ya ƙunshi kunya da kara da zumunta da sauransu. Idan kuwa aka rasa

waɗannan a cikin al'umma tabbas wannan al'umma raunanna ce.

3. Takun Saƙa da addini: A fannin nazarin al'adun Hausawa akwai kiɗe-kiɗe da raye-raye. Waɗannan bubuwa da ake nazari a al'adun Hausawa, wasu ganin suna takun saƙa da koyarwar addinin Musulunci. Tasirin Musulunci ya hana wasu Hausawa ganin ƙimar da hikimar nazarin al'adun Hausawa a makarantu, wanda yin hakan suna ganin tamkar saɓo ne (Bunza, 2015). Hakan babban ƙalubale ga Hausawa masu sha'awar nazarin Hausa, kasancewarsu masu tsananin riƙo da addininsu. Wannan ya kawo cikas a nazarin Hausa a ƙasar Hausa inda ake kallon duk wani mai nazarin al'adun Hausawa a matsayin mutum wanda yake raya al'adu masu takun-saƙa da aƙidodin addinin Musulunci, don haka da yawan Hausawa suka ƙaurace wa nazarin al'adun Hausawa a makarantu daban-daban.
4. Ƙarancin Wuraren Adana Kayan Tarihi Na Al'adun Hausa: Da yawa daga cikin kayan tarihi na al'adun gargajiyar Bahaushe babu wurin adana su a mafi yawan makarantun ƙasar Hausa. Samar da wuraren adana kayayyakin tarihi na al'adun Hausa zai taimaka wajen adana tarihi na ayyukan da magabata suka gudanar, wannan ya yi daidai da ra'ayin (Popoola, 2018:64) inda ya bayyana muhimmancin wuraren adana tarihi a ɓagaren nazarin al'adun Hausa domin tattara kayan tarihi saboda faɗakarwa da ilimantar da na baya game da ayyukan da magabata suka gudanar masu ƙima. Samar da irin waɗannan wurare zai bunƙasa nazarin al'adu a aikace tare da samar da hanyoyin da za bi a ingata wasu ayyuka domin ci gaba da more masu. Nazarin al'adun Hausawa a ƙunshi nishaɗantarwa. Kusan dukkan al'amurran al'ada ɗauke suke da nishaɗantarwa, saboda mafi yawancin al'amurran da al'umma ke aiwatarwa ƙunshe suke da bukukuwa Haka kuma bukukuwan nan ana aiwatar da su ne ta hanyar kiɗe-kiɗe da bushe-bushe da waƙe-waƙe da wasanni da sauransu (Yakasai, 2012:36). Rashin wuraren adana kayayyakin al'adun Hausawa kan rage nishaɗin yadda za a nuna ma masu koyo wasu abubuwan da aka yi amfani da su a da wajen yin kaɗe-kaɗe da sauransu. Abin da dalibai suka sani kawai shi ne sunayensu a faɗe, amma ba za su iya nuna su a zahiri ba. Wannan ba ƙaramin ƙalubale ba ne a fagen nazarin al'adun Hausawa.
5. Ɗabi'un Wasu Malaman Hausa: A lamarin nazari da koyar da al'adun Hausa ya kamata malami ya tsaya ya koyar da al'adun Hausawa ga ɗalibai kamar yadda ya kamata. Sai dai kash! Wasu malamai ba su ɗauki aikin su da muhimmanci ba, saboda haka abin da suke yi a wurin aikin shi ne amaja (Salihi, 2005:17). Abun ban haushi da takaici shi ne, wannan dabi'a na faruwa har yanzu a cikin makarantunmu a ɓangaren Hausa. A wasu lokuta za a taras da malami bai

koya wa ɗalibai komai ba a tsawon zangon karatu, kullum ya shiga aji sai ya ba ɗalibai labaran da ba su da alaƙa da abin da aka tsara a koyar da su, da zarar lokaci ya yi sai malamin ya fice daga cikin aji. Wannan ɗabi'a ba za ta bari nazarin al'adun Hausawa su ci gaba ba Bunza, (2007) ya bayyana rashin sanin ciwon kai, da rashin adalci da wofintar da kai da bayar da gaba baya ga malamin Hausa ko ɗalibin da ba ya kishin abin da yake yi. Masu irin wannan halin suke rusa Hausa da karatun Hausa, sannan kuma za ka tarar da irin waɗannan malaman ba su fahimci Hausar ba, don haka ba su da wani abu da za su koya wa dalibansu. A ƙarshe sai a yi haihuwar guzuma ɗa kwance uwa kwance. Masu irin wannan ɗabi'a su ne suke shiga farfajiyar karatun Hausa a munafunce ba su kaunar Hausawa balle Hausa kuma ga su da ita suke cin abinci kuma ko'na aka san su domin ita ne, a taƙaice Hausa ta yi masu riga da wando.

6. Nunin Hausa da al'adun Hausa da hannun hagu: A kan samu wasu Hausawa da ba su fahimci Hausa da al'adunta ba suna yi mata nuni da hannun hagu, wannan na cikin ƙalubale da nazarin al'adun Hausawa ke fuskanta Bunza, (2007:4) ya bayyana cewa wasu Hausawa `yan boko waɗanda ba su ƙoshi da karatu kuma sun kasa fahimtar hikimar nazarin Hausa da al'adun Hausa suna nuni ga harshensu na gado da al'adunsu da hannun hagu. Babbar illar da irin waɗannan mutane suke yi wa nazarin al'adun Hausawa a makarantu shi ne suna kallon duk wani mai karatun Hausa a matsayin rago, wanda bai fita daga cikin harshen da kowa ya sani ba. Haka kuma sukan yi ƙokarin karya wa sabbin ɗalibai guiwa masu sha'awar nazarin Hausa da al'adunta. Saboda suna ganin cewa duk wanda ya karanci Hausa babu wani aiki da zai yi illa koyarwa. Sannan kuma ƙoƙarin neman kujerar ci da ceto da babakere da dukiyar talakawa ya sa wasu dalibai sun ƙauracewa Hausa da al'adun Hausawa a matakin karatu daban-daban. Wannan ya sa Alhaji Aƙilu Aliyu yake cewa a cikin waƙarsa kamar haka:

"Kowa da yare nasa bai ƙyama tai,
Mu ga mu mun tozarta harshen Hausa.
Wai don gadarar mun jiyo Turanci,
Har ba mu son magana da harshen Hausa.
Tsuntsu kamata yai da shi ya yi kuka
Ya irin kaka nasa can mai nisa".

(Aƙilu Aliyu: Waƙar Hausa Mai Ban Haushi)

Waɗannan baitoci na Alhaji Aƙilu Aliyu suna nuna mana yadda Bahaushe bai ɗauki harshen Hausa da al'adun Hausawa da muhmmanci ba. Mawaƙin ya ba da shawara da cewa ya dace a ce Bahaushe ya riƙe harshensa da al'dunsa da kyau, amma har yanzu Hausa da al'adun Hausawa suna fuskantar ƙyama a wurin Hausawa na asali musamman wadanda suka nazarci wani fanni na Turanci. Wannan babbar nakasu ne wajen nazarin al'adun Hausa.

## Sakamakon Bincike

Wannan bincike ya fahimci cewa nazarin al'adu Hausawa yana fuskantar matsaloli da dama waɗanda idan ba a tashi tsaye aka yaƙe su ba za su daƙushe haske da kwarjinin da Allah ya ba wa wannan fanni. Daga cikin abin da bincike ya gano cewa ana cusa wa Hausawa harshe da al'adun Turawa a makarantu. Sannan kuma binciken ya fahimci cewa tilasta harshen Ingilishi da al'adun Hausawa a makarantun tamkar tauye haƙƙin ɗan'adam ne. Haka kuma binciken ya fahiimci cewa al'adun baƙin al'ummu sun yi tasiri ƙwarai ga ɗalibanmu wanda hakan yake bayyana a wajen irin suturar da suke sawa da waƙoƙi da suke sauraro da sauransu. Binciken ya gano cewa, nazarin al'adun Hausawa na kamuwa da cikas a hannun malaman addinin Musulunci waɗanda yake kallon nazarin al'adu tamkar raya wasu al'adu ne dake takun saƙa da Musulunci. Wannan ya sa da yawa daga cikin Hausawa suka ƙaurace wa nazarin, kasacewar akasarin Hausawa Musulmi ne kuma suna da tsaninin riƙo da shi. Bugu da ƙari, binciken ya gano cewa akwai ƙaranci wurin adana kayyakain al'adun Hausawa a makarantu (meseum). Rashin wurin adana kayyakin da suka shafi al'adun Hauswa yana zama barazana a wurin nazarinsa. Haka kuma binciken ya fahimci cewa ɗabi'un wasu malaman Hausa yana takura nazarin al'adun Hausawa a makarantu, mafi yawancin irin waɗannan malamai ba su ɗauki aikinsu da muhimmanci ba haka kuma ba su san ƙimar abin da suke koyarwa ba domin haka ba su ba shi daraja. Bincike ya gano cewa wasu Hausawa ba su nuna kishin harshen nasu da al'adunsu. Don haka irin waɗannan mutane babbar barazana ce ga nazarin al'adun Hausawa.

## Shawarwari

Hausawa sukan ce, shawara ɗaukar ɗaki. daga cikin shawarwarin da wannan bincike yake so ya bayar sun haɗa da:

i. A inganta koyar da Hausa da nazarin al'adun Hausawa, yadda za a cusa wa ɗalibai son kyawan al'adun gargajiya waɗanda suka ƙunshi gaskiya da riƙon amana da zumunta da adalci da sauransu. Haka kuma a nuna wa ɗalibai amfanin kula al'adun gargajiya da riƙo da su musamman abin da ya shafi sutura. Sannan su ma Malamai su riƙa shiga mai kyau yadda za su zama abin koyi ga ɗalibai.

ii. Manyan malamai da shehunan Hausa su tashi tsaye su yaƙi aƙidar hana yin Hausa a cikin aji Su tabbatar da sun ga bayar wannan guba da Turawan mulkin mallaka suka dasa a zukatanmu. Sannan su himmatu wajen saka darussa da jiɓanci kimiyya da fasaha a cikin harshen Hausa ta yadda matasanmu za su riƙi abin da muhimmanci Manyan masana su ƙara ƙokarin bincike a harshen Hausa da al'adunta ta yadda harshen zai bunkasa ya kuma zama harshen ƙasa.

iii. A riƙa shirya taron wayar wa jama'a kai game da nazarin al'adun Hausawa ta yadda za su daina ƙyamarsu tare da kallon suna yi addinin Musulunci karan tsaye.

iv. A riƙa shirya taron bita da ƙara wa juna sani a kai a kai dangane da abin

da ya shafi harshen Hausa da al'adun Hausa, musamman irin ci gaban da aka samu da kuma inda aka fuskanta.

v. Samar da ɗakunan ajiyar kayan gargajiya na tarihin Hausawa a makaratu. Yin haka zai hana salwancewar su kuma zai sauƙaƙa nazarin al'adun Hausawa.

vi. Akwai buƙatar a nuna wa Hausawa `yan boko kishin harshen Hausa da al'adun Hausawa ta yadda za su kare martabar gadonsu a duk inda suke.

## Kammalawa

Wannan takarda ta tattauna ƙalubalen da nazarin al'adun Hausawa da masu nazarinsu ke fuskanta a tsarin ilimin Nijeriya. Takardar ta fara da fito da ƙalubalen da wasu baƙin al'umma suka ɗarsa guba a cikin zuciyar Hausawa da yadda suka nuna fifikon harshensu da al'adunsu. Sannan an leƙo ƙalubale da nazarin al'adun Hausawa ke fuskanta ta fuskar ɗabi'un malaman Hausa da kuma ɗabi'un wasu Hausawa `yan boko waɗanda suke wuƙalatar da harshen Hausa da al'adun Hausawa. Rashin wuraren adana al'adun Hausawa a makarantu na daga cikin ƙalubalen da binciken ya hasko. Daga ƙarshe, binciken ya ba da shawarwari a kan yadda za a shawo kan waɗannan ƙalubale domin kwalliya ta biya kuɗin sabulu.

## Manazarta


Adeyanju, T.K etal, (2019). Curriculum in Nigerian Languages for Schools and Training Colleges. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Ado, A. (2019). *Ra'in Bincike Kan Al'adun Hausawa.* Katsina: Government Printing Press.

Amin, N. (2015). "Baƙin Dole: Nason Al"adun Turawa Ga Al'adun Hausawa A Lardin Sakkwato da Gwandu da Argungu, 1903-2010." Kundin Digiri na uku. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Danfodiyo.

Bakura, A. R. (2018). Leƙen Asirin Turawa da Ginuwar Labarin Hausa. A cikin Labarin Hausa a Rubuce (1927-2018) edited by Malumfashi, I. Zaria: Ahmadu Bello University Press. Pg 37-58.

Bunza, A. M. (2022). Diwanin Masu Karatun Hausa. Takadar da aka gabatar a taro Ƙaddamar da Ƙungiyar Hausa A Kwalejin JFLA da ke Minna.

Bunza, A.M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Nigeria Limited.

Bunza, A.M. (2007). Hausa A Idon Duniya. Muƙalar da aka gabatar a Mujallar Makarantar Hausam Sokoto.

Bunza, A.M. (2018). Karatun Hausa A Farfajiyar Karatun Boko (Tafiya da Waiwaye Maganin Mantuwa) A Cikin *Topical Issues In Language Studies* Edited by Wamba, B.Y etal a publicacation of Hausa Department Federal College of Education, Kontagora Pp 1-12

Federal Reublic of Nigeria, (2013). National Policy on Education. Lagos: Nigeria. NERDC Press.

Fafunwa, A.B. (1992). *Educational Project.*(1970-1976).Ibadan University press.

Muhammad, D.(Edita) (1980). *Fasaha Akiliya.* Zaria: Northern Nigeria Publishimg Company.

Niyi, O.O & Apokere, R.U & Salihu, H. (2025). Imlementation of Indigeneous Language Policy For Basic Science and Mathematics in Niger State, Nigeria Challenges and Prosects A ublication of *British*

*Jouranal of PschologyResearch,* 12 (3) 23-31.

Nutli, T.G. & Mudau, A.V.(2024). Influence of an African Indigeneous Language on Classroom Interaction and Discourse. Edu. Sci., 14, 684, https://doi/10.3390edusci14070684.

Poopola, J.O. (2018). "The Significant of Cultural Institution to National Development: The Case Study of National Meseums" in *Topical Issues In Language Studies* Edited by Wamba, B.Y etal a publicacation of Hausa Department Federal College of Education, Kontagora Pp 62

Salihim T.M. (2005). *Waiwaye A Kan Aikin Koyarwa.*Kano: TSC Computer Services.

Sallau, B.A.(2018). "Tarɓarɓarewar Al"adun Hausawa a Jami'o'in Arewacin Nijeriya: Ƙalubale ga Tsarin Koyo da Koyarwa a ƙarni na 21. A cikin *Kadauara Journal of Hausa Multidiscilinary Studies.* Vol. 1 No. 4 Secial Edition Kaduna State University. www.amsoshi.com Retrieved on 18/04/2025.

Usman, B. (2013). *Folklore and History: The Twin River of The World Heritage.* Abuja: Klaida Communication Limited.

Yakasai, S.A. (2012). *Jagoran Ilimin Walwalar Harshe.* Sokoto: Garkuwa Media Services.

Yakasai, S.A. (2014). *Language and Cultural Preservation: Hausa in Face of Technological Advancement.* Kano: Gidan Dabino Publishers.